# KYAUTAR ƘAHO A FADAR FULANI: TSOKACI DAGA FADAR KANO

**Halima Daura Kabir**
Sashen Harsuna da Al'adun Afirka
Tsangayar Fasaha
Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria- Nijeriya.

**Abstract**

January 30th 2023 marks the last Presidential Visit of President Muhammadu Buhari to Kano State and Kano Palace as well. While in Kano, the President commissioned some states projects and paid homage to the Emir of Kano, Alhaji Aminu Ado Bayero, where he also commissioned a renovated mini palace called 'Soron Ingila'; which was formally built by the eight Fulani Emir of Kano, Malam Muhammadu Abbas. As part of the tradition, the Emir presented a gift of cow horn to Mr. President which culminates into social media responses. The paper adopts historiography and interview as a source of collecting data to examine the meaning and value of gift of horn to an important dignitary in Fulɓe tradition. Findings of the research reveals how the horn was used for centuries to keep valuable items inside; such as money and bullan (traditional attire among the ruling class that was inside the horn presented to the President), and for decoration which many people including some Fulani young ones are ignorant and perhaps the reasons for the debate.

## 1.1 Gabatarwa

Shugaban ƙasa Muhammadu Buhari ya kai ziyarar aiki na kwana ɗaya a jihar Kano ranar Litinin 30th Jan. 2023, domin ƙaddamar da wasu ayyuka da suka haɗa da: buɗe tashar fiton kayayyaki na nesa da teku da sabuwar tashar lantarki mai amfani da albarkatun ruwa da babbar gadar sama ta titin zuwa Maiduguri da kuma babbar cibiyar amfani da fasahar zamani. Shugaban Ƙasa ya kuma kai ziyarar ban girma ga Mai Martaba Sarkin Kano, Alhaji Aminu Ado Bayero, a inda nan ma ya ƙaddamar da wata tsohuwar majalisa da aka daɗe ana yi mata kwaskwarima tun zamanin Sarki Abbas, wato 'Soron Ingila'. Kamar yadda yake ga al'adar Saraki ta karimci, Sarki ya yi wa Shugaban Ƙasa kyautar ƙaho na alfarma. Sarakuna mutane ne masu karimci matuƙa, musamman ga baƙi da maroƙa da ma sauran al'ummar gari. Sarakuna na nuna karimcinsu ga baƙi da kuma girmama su ta hanyar yi masu kyauta. Sukan samar musu masauki da abinci mai kyau da sutura, har ma da kuɗi, idan suka daɗe a haɗa da gona. A kuma yi masu aure idan ba su da mata. Wannan ya sa baƙi da dama suka zama 'yan gida a Ƙasashen Hausa. Ga al'ada Sarakunan Fulani suna karrama baƙi da kyautar bajimi ko tufafi, alalmisali rigar alfarma da aka fi sani da *bullan*, wadda kuma ake adana ta a cikin ƙahon shanu. Sa ya kasance babban abin da Bafulatani yake alfahari da shi, domin haka yake ganin ƙimarsa ko darajarsa fiye da komai a doron ƙasa. Wannan dalili ne ya sa babbar kyautar Fulani ga babban baƙo, musamman a fada ba ta wuce bajimin sa da suturarsu ta ƙure adaka (*bullan*). A iya cewa duk wanda Sarakunan Fulani suka ba ɗaya daga cikin wannan nau'i na kyauta ba ƙaramin muhimmanci yake da shi ba, ba kuma ƙaramar sa'a ya taka ba. Irin wannan kyauta ce Shugaban Ƙasa Muhammadu Buhari ya samu daga Mai Martaba Sarkin Kano, Alhaji Aminu Ado Bayero, a ziyararsa ta ranar 30th January, 2023. Shugaba Buhari ya samu kyautar *bullan* wadda take a cikin ƙaho. Kodayake jama'a da dama, sun yi ƙorafi musamman a dandalin sadarwa na sada zumunta, saboda rashin sanin sirrin da ke cikin wannan ƙaho. Masu iya magana na cewa, "Rashin sani, karen gwauro ya kori bazawara". Jama'a da dama sun tofa albarkacin bakinsu kan wannan kyauta, da dama suna ganin kamar ƙasaƙanci ne a yi wa Shugaban Kasa sukutum kyautar ƙaho! Wannan dalili ya haifar da yin tsokaci a kan wannan kyauta domin gano ma'ana da hikimar sa rigar *bullan* a cikin ƙaho, saboda la'akari da cewa jama'a da dama, har ma da wasu Fulanin ba su san wannan al'ada ba.

### 2.1 Fada a Ƙasar Hausa

*Kamusun Hausa* (2006:129) ya bayyana ma'anar fada da ma'anoni guda uku: i. majalisar Sarki inda ake taro ana kai masa gaisuwa ii. gidan Sarki da kewayensa iii. samun shiga, musamman ga wani babba. A yayin da Mazawaje (1985:1) ya ce fada wuri ne na zartar da hukunci, kamar kuma yadda Hauwa (2008:66-67) ta yi ƙarin bayani da cewa, fada wuri ne na gudanar da mulki inda Sarki yake shugaban majalisa, sai Waziri da sauran manyan mutane masu riƙe da muƙamai daban-daban waɗanda suka haɗu suka kafa majalisar zartarwa. Wannan ma'ana na nuni da cewa a fada, musamman ta Ƙasar Hausa akwai 'yan majalisa da ke taimakawa Sarki gudanar da mulki. Wannan ya sa ake cewa, "Ba a mugun Sarki sai mugun bafade". A taƙaice a iya cewa fada haraba ce ta mulkin Sarki a duk inda yake, kuma nan ne muhallinsa ko tushen masarauta. Fada wuri ne na bayar da umarni, saboda haka ba gini ba ne fada, ko gari ko birni ko daji, wurin da Sarki ya sauka, to nan ma fada ce, domin nan ma za a iya zartar da hukunci da kafa aƙida. Masu iya magana na cewa, "Fada gidan ban kashi". Wannan magana babu shakka haka take saboda fada wuri ne na gyaran tarbiyya. Fada kotu ce ko wurin shari'a, shi ya sa ma ake da Alkalin Garka da Yari da Liman da ke haɗa gwiwa ƙarƙashin shugabancin Sarki su zartar da hukunci. A fada ake ba mai hakki, hakkinsa, a hukunta mai laifi daidai laifinsa. Sannan a nan ake sasanta jama'a da sauran makamantan haka.

#### 2.1.2 Fadar Kano

Masarautar Kano ta dawo hannun Fulani masu jihadi daga Sarakunan Haɓe a shekara ta 1807. Malam Sulaiman shi ne Sarkin Fulani na farko bayan masu jihadi sun tuɓe Sarki Alwali daga sarauta. A bayanin masana tarihi, Fulani sun yi ƙaura daga ƙasashensu na asali zuwa Ƙasar Hausa saboda dalilai guda biyu ko uku. Dalili na farko shi ne domin samun wadataccen makiiyayi ga dabbobi, na biyu saboda yaɗa addinin Musulunci. Sallau (2009:144) ya ƙara da cewa ɗabi'un Hausawa kyawawa na zama lafiya da karrama baƙi ya taimaka wajen tururuwar al'ummomi da dama tare da mayar da Ƙasar Hausa gida a gare su. Masana irin su Abubakar (1977) da Baƙo (1990) da Maishanu (2009) da saura da dama sun bayyana cewa ba za a iya tabbatar da lokacin da Fulani suka fara shigowa Ƙasar Hausa ba, kodayake ana kyautata zaton sun shigo ne a tsakanin ƙarni na 13-14. Abubakar (1977) ya ci gaba da cewa ƙasar Senegal ta Afirka ta Yamma ce mazauninsu na farko kafin su bazu zuwa ƙasashen Chadi da Gambiya da Habasha da Kamaru da kuma Sudan. A nasa ra'ayin, Maishanu (2009) cewa ya yi, gano takamaiman lokacin hijirar Fulani daga mazauninsu na farko kafin su shigo Arewacin Nijeriya, abu ne muhimmi da masana, musamman na tarihin ba su mayar da hankali a kan sa ba. A dalilin haka ne masanin ya yi amfani da wata zuriyar Fulani mai suna 'Wolarɓe' domin bin diddigin asalin Fulani da lokacin da suka fara shigowa yankin Ƙasar Hausa. Sakamkon binciken ya bayyana cewa danganta asalin Fulani daga zuriyar Uqba Ibn Amr, sha-ci- faɗi ne, sai dai a ce dangantaka ta addinin Musulunci. Domin haka ya ce tun a ƙarni na goma sha ɗaya (11thc) Fulani suka bazu a Daular Ghana kafin su shigo Ƙasar Hausa. Baƙo (1990) ya yi tabbaci da cewa Fulani sun shigo ƙasar Kano ne a lokacin mulkin Sarkin Kano Yakubu (1452-1462), inda suka fara yada zango a wasu wurare irin su Dambatta da Kazaure da Rano da kuma Sumaila.

Ƙasar Hausa a yau tana ƙarƙashin mulkin Sarakuna Fulani, idan aka cire Daura da sarauta ta dawo hannun Haɓe a shekara ta 1907. Daga Sarkin Kano Sulaiman Dabo zuwa yau, an yi Sarakunan Fulani guda goma sha biyar (15). A yanzu Sarki Aminu Ado Bayero ke gadon sarauta kuma ya gada daga mahaifinsa, marigayi Alhaji Ado Bayero.

Idan aka yi la'akarin karimcin Sarakunan Ƙasar Hausa, za a iya cewa wannan kyauta da Sarkin Kano Aminu Ado Bayero ya ba Shugaban Ƙasa Buhari, ba abin mamaki ba ne domin ya gaji gidansu. Har ila yau, karimci na daga cikin kyawawan ɗabi'un Basarake (Hausa / Fulani). Wannan ya tabbata da irin yabon kyauta da maroƙa suka yi wa marigayi Sarki Ado Bayero a waƙoƙi da kirarin da aka yi masa a lokacin da yake raye. Marigayi Musa Ɗanƙwairo Maradun, a waƙarsa ta 'ba takura kaurin gaba', yana cewa:

Jagora: Aljannar duniya,
'Y/Amshi: Ɗan Abdulƙadir Sarki Ado,
: Na tare da kai ya lilwanta,
: Ruwan wankin dauɗa,
: Alhaji ruwan wankin dauɗa ne.

Jagora: Sarki mai kyautar doki,
: Sarki mai kyautar riguna,
: Sarki mai kyautar wanduna,
: Sarki mai kyautar kuftoci,
: Sarki mai kyautar alkyabba,
: Sarki mai kyautar rawuuna,
: In dai yai maka kayan ƙawa,
: Ya mika ma kuɗɗi fam ɗari,
Y / Amshi : Abin shagali ya samu...

(Gusau 2009: 89-90).

Musa Ɗanƙwairo ya kira Mai Martaba Sarki Ado Bayero, *'aljannar duniya'*. Ma'ana, wuri mai daɗi, mai ni'ima, kamar yadda Dikko da Macciɗo (1991:3) suka bayyana. Aljanna wuri ne da duk wani mahaluki yake fatan ta kasance makomarsa saboda ni'imominta da jin daɗinta tamkar yadda addinin Musulunci ya kwaɗaita mana. Ya kuma kira shi *'ruwan wankin dauda'*, wato mutum (basarake) mai wanke talauci domin duk wanda yake tare da shi muddin ya yi masa kyauta, to ba ƙaramar kyauta ba ce. Kyauta ce da ke kauda larurori da dama, tamkar yadda ruwa ke wanke dauɗa. Ɗanƙwairo ya kuma lissafo ire-iren abubuwan da yake kyauta da su da suka haɗa da: kuɗi da riguna da alkyabba da rawuna da makamantansu. Babu shakka, masu iya magana kan ce, "Kyan ɗa ya gaji gidansu". Sarki Aminu Ado Bayero ya gaji gidansu da irin wannan kyauta da ya yi wa Shugaban Ƙasa Muhammadu Buhari..

**3.1 Kyautar Ƙaho**

Ƙaho suna ne na jinsin namiji, jam'insa kuma 'kahonni ko kahunhuna'. *Kamusun Hausa* (2006: 273) ya bayyana ma'anar ƙaho kamar haka: i. wani ƙashi da yawanci guda biyu ne da kan fito a kan dabba, misali saniya ko rago ko akuya ko kuma barewa. ii. tsattsaga jiki domin fitar da jini da wanzamai ke yi wa mara lafiya ta hanyar amfani da ƙaho. iii. *ƙahon barewa*, wata kuɓewa mai dogon 'ya'ya. iv. kafaffan mutum ko marowaci. Ma'ana ta farko ita ce ake magana a wannan nazari, wato ƙahon dabba, dabbar ma ta nau'in shanu. A yi kyauta shi ne a ba wani mutum wani domin ra'ayi, ko son kai, ba tare da ya yi wani aiki ba. Ana kyauta a tsakanin jama'a domin tana ƙara ɗorewar zumunci da tausayawa juna da kuma girmamawa. Kyauta tana ƙara danƙon ƙauna a tsakanin al'umma, misali a tsakanin ma'aurata ko masoya ko tsakanin babba da yaro ko shugaba da mabiyansa. Kyauta na ɗaya daga cikin ɗabi'un da ake so babba ya kasance yana da ita, domin ita ce halin girma a tsakaninsa da na ƙasa da shi. Saboda haka duk babban da ya kasance hannunsa a buɗe yake akodayaushe, to zai zama abin so da ƙauna. Kyauta a tsakanin babba da mabiyansa hanya ce ta tausayawa da kulawa. Wannan ya sa masu iya magana suka ce, "Laifin babba rowa, laifin yaro ƙwiwa. Ke nan, kamar yadda ake so babba ya kasance yana yi wa na ƙasa da shi kyauta, ana kuma fata ƙarami ya mayar da kyautar da ladabi da biyayya.

Sana'ar Fulani, musamman ta asali ita ce kiwon dabbobi (shanu da sauran dabbobi na gida irin su tumaki da awaki), domin haka saniya muhimmin abu ce ga Fulani. Bafulatani na darajta saniya fiye da ƙima saboda ita ce dukiyarsa. Dukiya kuma ba abin wasa ba ce ga kowane mahaluki a doron ƙasa, sai dai wanda ba shi da cikakken hankali ko yaro ƙarami. Yadda Bafulatani ke fifita saniya a rayuwarsa, a iya cewa kamar ya fi ɗan cikinsa martaba, wannan ya sa ƙahon sa ma yake da ƙima a wurinsa. Shi ya sa yake naɗe kyautar isa zuwa ga isassu a cikin ƙaho. Masu iya magana na cewa, "Abun cikin ƙwai ya fi ƙwan daɗi". A hirar da aka yi da wani Bafulatani, ya bayyana dangantakar saniya da Bafulatani ya tabbatar da yake cewa:

"Muhimmancin saniya ga Bafulatani lamari ne mai girman gaske. Domin saboda muhimmancin shanu ne gaba ɗaya Bafulatani ya sadaukar da rayuwarsa a kan jin daɗin su, maimakon jin daɗin shi kan sa. Da farko, idan aka yi la'akari da mazaunin Bafulatani, musamman makiyayi, a ina yake zama? Zaman da yake yawanci a daji ne, domin me yake zama a daji a maimakon birni? A birni ake samun abubuwan more rayuwa, irin su lantarki da tituna masu kyau da sauransu. Ga kasuwanni, kaya da sauran abubuwa, komai cikin sauƙi, amma ya yarda ya zauna daji. Idan ma yana neman wani abu sai ya yi tafiya mai nisan zango kafin ya samu. Duk waɗannan ba su dame shi ba, saboda jin daɗin dabbobinsa, a wurinsa shi ne nasa. Wato lamarin shanu ga Bafulatani, idan babu su tamkar shi ma rayuwarsa ba ta cika ba.

A lura da muhallin da yake, muhallin da yake yawanci yana yin sa na wucin- gadi, duk saboda dabbobinsa, domin a tunaninsa, duk inda ya zauna bai ga ci gaba ga waɗannan dabbobin nasa ba, to gaskiya wannan wuri ba wurin zama ba ne. Gaba

CC BY-NC-ND

zai yi ya nemo wurin da yake ganin ya fiye wa dabbbobin nasa samun jin daɗi fiye da inda ya baro.

Baya ga muhalli ma, a duk lokacin da ya tashi zuwa kiwo, da ruwa da iska da komi duk ba za su sa ya dawo ya fake a wannan muhalli ba, a'a, dole yana can tare da dabbobin nan. Domin komai ruwa da iska ko sanyi, ba zai sa ya dawo da dabbobin nan rana tsaka ya fake ba. A'a, ba zai yi ba! Ya yarda ya sadaukar da rayuwarsa gaba ɗayanta, ya sha wahala, ruwa ya yi masa duka, sanyi ya yi yayinsa a kansa ba tare da ya fake ba, duk da yake ya san cewa halittarsa ta bambanta da ta dabbobi. Su sun fi shi jure waɗannan abubuwa da na ambato, amma bai dame shi ba.Tun da dai yana yin haka ne domin jin daɗin su, bai damu da kansa ba. A lura kuma, shi fa Bafulatani ya ɗauka cewa, in dai mutum ba shi da shanu, kamar ba Bafulatani ba ne, kamar ma ba ya cikin su. Domin haka ma Bahaushe ya kafa hujja da wannan.Ya yi karin magana da ke cewa, "*Shiga sharu ba shanu*". Shiga sharun da ake faɗa na nufin wata al'ada ta Fulani ta shaɗi. Ina kai, ina shiga al'adar da kai ba ka cikin wannan al'umma? Ma'ana, idan kai ba Bafulatani ba ne, bai kamata ka yi sharu ba, ko ka yi shaɗi. Amma da ya tashi bai ce, 'shiga sharu ga wanda ba Bafulatani ba', sai ya ce, 'shiga sharu ba shanu'. Ke nan, idan babu shanu ba Bafulatanin mutum yake ba, a tunanin wannan karin maganar. Gaskiya dangantakar Bafulatani da sa ko shanu abubuwa ne da yawa. Idan za a yi bayani dalla-dalla za a ɗauki lokaci mai tsawo, amma a taƙaice ke nan." (Dr. Adamu Shede).

### 3.2 Bukin Shayi

Ga al'adar Fulani, a lokaci da aka yi wa yara maza kaciya suka warke ana bikin *'nastordo'*. Nastordo na nufin bukin maraba da waɗanda aka yi wa shayi. A al'adance akan tara yara kamar huɗu ko fiye masu shekara 7-10 a yi masu kaciya rana guda. Akan yi masu bukka can nesa da gida, inda za su riƙa kwana saboda pulaaku na Bafulatani, wato alkunya kasancewa yaran ba su sanya wando a lokacin. Bayan sun warke, ana shirya babban buki domin tarbar su zuwa gida. A lokacin bukin ana tanadar kayan ciye-ciye da shaye-shaye, ana kuma da raye-raye da waƙe-waƙe da kirari (kowa irin na gidansu, misali idan kakanni suka kasance jarumai ko masu kyauta da makamantan haka). A wannan rana ce za su yi wanka sannan su sa sababbbin kaya. Dangin da abokanan arziki, musamman kakanni suna tanadar kyaututtuka daban-daban, kama daga tumaki da awaki da shanu da kuɗaɗe domin su ba su. Wasu ma a ranar ce ake ba su mata (ta aure), kuma maganar ta zauna har abada, muddin ana raye. Wannan buki an fi gudanar da shi a yankin ƙasar Adamawa da kewaye, zuwa ƙasar Kamaru. A kuma wannan rana ce ake yi masu aski (ko da kuwa akwai kitso a kansu, kasancewa Fulani mazansu da matansu kan yi kitso). Bayan an aske kan sukan rataya ƙaho ɗaya ko biyu a wuyansu. Sannan su sa wasu ƙahonni uku a ka, ɗaya ya kalli goshi sauran biyun su sauka a kunnuwa dama da hagu. Wannan kwalliya ta ƙaho ana kiran ta *'baggel / mbaggon'* da Fulatanci ((tilo / jam'i) Ke nan, wannan al'ada na nuna muhimmancin sa ga Bafulatani domin ƙahon na wakiltar sa. Har ila yau, a al'adance hikimar ɗaukan ƙahon a ka da rataya shi a wuya yana alamta sun zama cikakkun mutane waɗanda za su iya mu'amula da shanu a kodayaushe kuma a ko'ina. A baya, daga wannan lokaci ne za a iya ba su shanu su tafi kiwo ba tare da wani babba ba.

### 3.3 Ado

Ado ko kwalliya na ɗaya daga cikin abubuwan da ke ƙara ƙawata wani abu ko wata halitta, musamman ta mutum da muhalli. A iya cewa a zahiri gaskiya ce kadai ba ta neman ado, kamar yadda Sa'adu Zungur yake cewa a waƙarsa ta 'Arewa Jumhuriya ko Mulukiya'(…gaskiya ba ta neman ado ko na daɗin muryar zabiya..). Al'ummar Fulani ta da can tana amfani da ƙahon sa domin kwalliya. Suna rataya shi a muhallinsu a matsayin ado domin ƙara masa kyau. Wannan ba ya rasa nasaba da yadda Bafulatani yake ba saniya daraja kuma yake alfahari da ita a matsayin dukiyarsa da kuma wani abu da yake tare da shi da ya kasance makwanci ƙadai ke raba su. Saboda haka ƙaho ma abin kwalliya ne ga Bafulatani domin yana tunƙaho da shi.

### 3.4 Magani

Ƙaho a al'dance ya kasance wani sinadari da ake amfani da shi a matsayin magani domin kariya daga miyagu. Masu bayar da maganin gargajiya suna bayar da magani da ake haɗa shi da ƙaho. Sukan bayar da wasu abubuwa da za a sa cikin ƙaho a rataya a kofar gida domin kariya daga barayi da mayu da makamantansu. A al'dance rataya wannan ƙaho yana hana duk wani nau'in

mugun abu shiga gida ko muhalli. Ko a gona ma wasu na rataya ƙaho domin ɓarayin gona, masu kwashe amfanin gona. Wanzamai ma suna fitar da jini gurɓatacce daga jikin marasa lafiya ta hanyar amfani da ƙaho, su yi masu ƙaho. A mafiyawancin lokuta ana ƙahon ne a baya ko a kirji. Wannan ya tabbatar da cewa ƙaho a al'adance sinadarin kariya ne daga miyagu kuma sindarin samar da lafiya ne. Domin haka, ko a fagen lafiya, *ƙaho* ba ƙaramin al'amari ba ne. Bugu da ƙari kuma, ƙaho makami ne domin yaƙar abokanan gaba, saboda dafinsa da tsirinsa duk wanda aka soka sai ya yi doguwar jinya ko ya halaka.

**3.5 Ajiya / Taska**

Masu iya magana na cewa, "Ajiya maganin wata rana". Al'ummar Fulani, musamman ta dauri, tana amfani da ƙaho domin adana abubuwa a cikinsa. Al'ummar Fulani sun lura da cewa ƙasa ba ta ruɓar da ƙaho ballantana ta lalata shi, domin haka suke sarrafa shi a matsayin taskar muhimman sinadaran rayuwa, irin su kuɗi da magunguna da sauran ƙaddarori masu daraja. Suna ajiyar kuɗaɗensu tun lokacin da ake amfani da wuri da kuma magunguna, duba da cewa zaman Fulani a daji ya sa sun san magungunan gargajiya. A wasu lokuta a kan sa wani abu cikin ƙaho a binne a matsayin doguwar ajiya. A masarautun Fulani akan tanaji manyan ƙahonni bajimin sa domin sanya kyautar alfarma a cikinsu. Babban misali shi ne irin kyautar da Sarkin Kano, Alhaji Aminu Ado Bayero, ya yi wa Shugaban Kasa Muhammadu Buhari kwanakin baya. Sarkin ya yi masa kyautar buki ta ƙure adaka a cikin ƙaho! Wannan kyauta ta tayar da ƙura, saboda ba kowa ya san abin da ke cikin ƙahon ba, amma al'ada ce ta Fulani na lokaci mai tsawo, su sanya wata kyauta ta musamman a cikin ƙaho. Mai Martaba Lamidon Adamawa, ya sha yi wa manyan baƙinsa irin wannan kyautar ƙaho, mai dauke da *bullan* a ciki, amma hankalin al'umma bai kai ga sanin wannan ba, sai yanzu da aka ba Shugaba Buhari. Kyautar ƙahon har ta kai an yi mata fassara na cewa, an ba shi ƙahon tashin kiyama ne. Wannan fassara ba ta rasa nasaba da takin-saƙa tsakanin al'ummar ƙasa da ta Fulani dangane da matsalar 'yan bindiga da kidnafin da suka taimaka wajen kushe wannan kyauta, musamman a kafafen sada zumunta na zamani.

**3.6 Ƙaho a Matsayin Kayan Kiɗa**

Makaɗa da maroƙa na busa ƙaho wajen samar da amo domin tsimawa da kambama gwanayensu saboda motsa jaruntakarsu. Alalmisali masu kaɗa take a wasu Masarautu na Kasar Hausa suna amfani da ƙaho wajen kaɗa taken Sarakuna, tamkar a Fadar Zazzau. Da ƙahon saniya ne ake amfani wajen kaɗa taken, bayan an yi masa huda guda uku a bakinsa. Sauran abubuwan da ake kaɗa take da su sun haɗa da algaita da tambari da farai da kakaki da makamantansu. To haka kuma, wasu makaɗa na amfani da ƙaho a matsayin ɗaya daga cikin kayan kiɗa. Yawanci ana amfani da busan kahon ne a kiɗan sarauta da na 'yan bori da farauta.

**3.7 Kafar Sadarwa**

Al'ummar Hausawa da Fulani suna amfani da ƙaho a matsayin kafar sadarwa ta musamman, domin isar da saƙonni. Suna amfani da ƙaho domin isar da saƙo ga 'yan'uwansu a lokacin da suke farauta ko yayin da suke kiwo a cikin daji. Misali, ana isar da saƙon cewa a karkata zuwa wata nahiya ko kuma daji ya ɓaci a kawo masu agaji. Domin haka ƙaho kafa ce ta sadarwa a tsakanin al'ummar Hausawa da Fulani.

**4.1 Rigar Bullan**

*Bullan* (/m) riga ce ta alfarma da Sarakuna da attajirai da manyan malaman zaure suke sanyawa. *Kamusun Hausa* (2006: ) ya bayyana *bullan* da cewa riga ce fara mai ƙananan ƙwarya-ƙwarya. A Fulatanci kuma *'buulan'* na da ma'anar iyo ko fito. A Kanuri kuwa idan an ce *'buullan'*, bajimin sa ke nan. *Bullan* babbar riga ce ta saƙar hannu wadda aka yin ta da zaren tsamiya kuma ake yi mata aiki kaɗan ba mai yawa ba, wato ana saƙa ta da zaren tsamiya.

**4.1.1 Nau'o'inta**

Ana hasashen cewa mutanen Kamaru ne suke ɗinka irin wannan riga kuma suke amfani da ita tun lokaci mai tsawo. Sannan kuma har yanzu zaren tsamiyar ma daga can ake samo shi. Kodayake yanzu an ce ana samun sa daga wasu ƙauyuka na ƙasar Kano, amma na Kamarun ya fi kyau da nagarta. Maɗinkanmu na gargajiya suke ɗinka *bullan* da hannu, wato aikin hannu ake yi mata. Wannan ya sa ɗinkin kan ɗauki lokaci mai tsawo saboda yana buƙatar natsuwa. Lokacin da za a ɗauka domin ɗinka *bullan* ya isa a ɗinka wasu riguna masu yawairin na ɗinkin injin. Wannan dalili ya sa rigar take da tsada matuƙa. Akwai kuma masu cewa *bullan*, riga ce ta Hausawa. To amma, har yanzu ana kawo ta daga Kamaru kuma

yanayin irin nasu ɗinkin ya ɗara na Husawa. Ko a sayarwa, *bullan* 'yar Kamaru ta fi ta Hausa tsada.

**4.1.2 Farashin *Bullan***

Masu iya magana kan ce, "Daidai kuɗinka daidai shagalinka". Kuɗin *bullan* yakan kama daga naira dubu ɗari ɗaya zuwa dubu ɗari bakwai, ya dai danganta da irin yadin da aka ɗinka ta da shi da kuma yawan zaren tsamiyar da aka yi amfani da shi. A baya can, a farin yadi ɗan Pakistan ake ɗinka *bullan* amma yanzu ana amfani da wagambari. A wani lokaci ma har da shadda mai tsada tare da la'akari da irin zaren da za a yi mata aiki da shi. Rigar *bullan* babbar riga ce mara nauyi saboda zaren tsamiya ba shi nauyi idan aka kwatanta shi da na kanti. Ana *aska biyu* a matsayin adon *bullan* (asake a yi masu zargu gaba da baya), kuma ɗinkin ba shi da kauri.

**4.1.3 Dangogin *Bullan***

Sauran manyan kaya da ake ɗinka su da zaren tsamiya sun haɗa da: *tokare* da *'yar Dikwa* da *kwaɗo* da *gafiya* da *aska tara* da *aska takwas* da *shabta* da *Bayero* da kuma *'yar Mubi*. Su ma kamar *bullan* riguna ne da saraki ke sawa, sai dai sun fi ta aiki. Misali, ana yi masu aiki gaba da baya da zaren tsamiya. Wannan ya sa tokare da shabta suka fi ta tsada kuma ko a cikin saraki, Sarakuna suka fi sa ta. Mata tsofaffi, a gida, suke sarrafa *kururun tsamiya*, ya koma zaren tsamiya, sannan su sayarwa maɗinka. A al'adance masu ɗinka manyan riguna na hannu suna naɗe su ne a ƙaranga. Haka kuma, ba a ɗinka kayan mata da wannan zare na tsamiya. Duk kuwa da kasancewarsa kayan ado na garari kuma matan ke sarrafa shi. Gas hi kuwa matan aka fi sani da ado, to amma ba sa ado da zaren tsamiya.

**5.1 Yadda Ake Samar da Zaren Tsamiya**

*Kururun tsamiya* ake sarrafawa domin a samar da zaren tsamiya kafin nan a yi ɗinki da shi. Ana samo *kururun tsamiyar* ne daga bishiyar tsamiya kuma musamman an fi samo shi daga wasu dazuzzuka na kasar Kamaru. *Kururun tsamiya* wata saƙa ce mai kama da saƙar gizo da wasu ƙwari da ake kira *kururu* (jam'i kuma *kururan tsamiya*), suke saƙawa a bishiyar tsamiya. Maza ne da suka shirya kan su suke shiga daji domin ɗebo *kururun* (kasancewa bishiyar tsamiyar kamar ta ce da kuka waɗanda aka camfe game da iskoki). Masu ciro *kururun tsamiya* sukan ciro saƙar baki ɗayanta ne da ƙwarin da ke cikinta, duk kuwa da cewa ba a buƙatarsu amma tsayawa a cire su zai ɓata lokaci. A lokacin da aka iso da *kururun* gida ana sa shi a wuta domin a dafa. A can baya babbar tukunyar ƙasa ake amfani da ita amma yanzu da masaki na ƙarfe wanda ake kira diro (*drum)* ake dafa *kururun tsamiya*. Wato dogon babban masaki da maƙera ke ƙerawa daga tama, irin wanda ake dafa ruwan wankan maijego da shi. Baya ga ruwa, ba a buƙatar komai domin dafa *kururun tsamiya*. Da zarar an tabbatar ya dahu, akan tafi da shi bayan gari a shanya shi a babban dutse domin ya tsane. A kan kuma barbaɗa masa toka (toka wadda aka kwashe da murhu bayan an kammala girki). A lokacin da *kururun* ya tsane, yakan koma kamar auduga, sai dai ya fi ta cizawa dangane da launi, sannan kuma ya fi auduga laushi a hannu. Daga nan sai a cura shi ƙanana a sa a ƙwarya, a kai kasuwa a sayar. To haka nan kuma wasu za su sara domin sayarwa, har dai ya kawo hannun mata masu kaɗi a gida. A yanzu saboda tasirin zamani, sukan sa curin *kururun* a leda. Ana sayar da curi ashirin naira dubu biyu da ɗari huɗu zuwa da ɗari biyar (2,400 / 2,500).

Mata tsofaffi da ke kaɗi su ne ke gyara wannan curi ta hanyar fitar da matattun *ƙwarin kururu* da ya rage a ciki da ma sauran tokar da ta yi saura a ciki. Mata masu kaɗi suna amfani da: taskira da faifai da alli da abawa da adudu da matari da mazari domin sarrafa wannan *kururun tsamiya* ya koma zare. A hirar da aka yi da Malama Adama, 'yar kimanin shekara saba'in da takwas da haihuwa; a gidanta da ke Unguwar Magajiya, Zariya, ta bayyana yadda suke sarrafawa da nawa suke sayar da zaren ga maɗunka. Malama Adama da ta kwashe shekara fiye da hamsin tana wannan sana'a ta kaɗi ta ce idan suka gyaran kururun ya koma kamar auduga, sai su tufka su kaɗa (ana sa tufka biyu domin a samu zare ɗaya kasancewa zaren tsamiya ya fi sauran zaren da aka sani kauri). Sannan sai su mayar da shi kamar zaren lagwani, da ake sawa a risho. Suna ɗaura kowane lagwani guda goma sha ɗaya su sayar da shi naira dubu biyu da ɗari (2,500) ga maɗunka.

**6.1 Sirrin Zaren Tsamiya**

Zaren tsamiya da ake ɗinka rigar *bullan* da shi, da ma wasu manyan riguna yana da ɗimbin sirri da ke tattare da kamar haka:

**6.1.1 Rashin Tsufa**

Babban sirrin da ke tattare da zaren tsamiya shi ne

ƙarko da nagarta da juriya. Zare ne da idan an yi ɗinki da shi kyansa ke ƙara fitowa ko bayyana zuwa lokacin da aka yi amfani da shi. Ma'ana, ana wanke shi kyawunsa na ƙara bayyana, musamman idan ya sha rana. Wannan ya sa idan aka yi ɗinki da wannan zare sai dai yadin ya tsufa ya bar adon da aka yi. Ke nan, zare ne a maimakon ya tsufa, ya lalace saboda tsawon lokaci da shiga ruwa, saboda wanki, amma kyawunsa ke ƙara bayyana a kullum. Wato abin nan ne da masu iya magana ke cewa, "Sayen na gari mayar da kuɗi gida".

**6.1.2 Alaƙa da Iskoki**

Zaren tsamiya zare ne na manyan mutane, musamman Sarakuna aka fi yi masu ɗinki da shi. A al'adance, kamar yadda ake kyautata zaton cewa, mai sanye da azurfa duk wani jifa da aka yi masa yana faɗawa a kanta ta yi baƙi, haka ma zaren tsamiya, mai sanye da shi an camfa duk wani surukulle da abokanan hamayya za su yi masa ba zai yi tasiri ba. Wannan ya sa Sarakuna ba sa rabuwa da tufafin da aka yi da zaren tsamiya, saboda ana la'akari da cewa suna da abokan hamayya, ko adawa, musamman waɗanda suka yi takara da su amma ba su samu ba, kuma suka ƙi yin biyayya / ba da hadin kai a tafi tare. Marigayi Sani Aliyu Ɗandawo a wata waƙarsa da yake ba 'ya'yan Sarki shawara yana cewa:

Jagora: Kai mutane ku baj jayayya,
: Ku yarda da ikon Allah,
: Allah shi ka bai, ya ba shi,
'Y/Amshi: Ku zo ku ruhwa mai baya
: Akwai gaba na nan ku ma,
: Ba duka za a zame Sarki ba.

(Gusau, S.M, 2009, Mai Yawuri Sabon Sarki).

Har ila yau kuma, kamar yadda zaren tsamiya ya kasance kariya ga masu sanye da shi, a wani gefen kuwa masu ɗebo shi daga daji, yake zamo masu akasi. Domin an camfa cewa, duk mai wannan sana'a ko shekara nawa ya yi yana yin ta, ba zai taɓa zama masa hanyar tara dukiya ko ya zama mashahurin mai kuɗi ba. Sai dai ya samu na rufin asiri, idan ma ya tara kuɗin ba za su amfane shi, sai dai su zamar kuɗin cizo ko na ajiya. Ko daga yanayin suturarsu za a ga haka, duk da kuɗinsu ba su sanya kaya na kamala ko na irin wanda yake samu ko yake da rufin asiri.

Haka zalika, duk masu sana'ar shiga daji domin ɗebo *kururun tsamiya*, a zahiri sukan kasance kamar wasu taɓaɓɓu., wato waɗanda iskoki suka shafe su. Ɗabi'unsu na zama irin na waɗanda ba su da cikakken hankali ko natsuwa. An camfa cewa, wannan ba ya rasa nasaba da iskokin da ke tattare da bishiyar tsamiyar da suke ɗebo *kururan* sukan shige su. An kuma ce wai alhakin kuraran da suke raba su da muhallinsu da kuma kashe su ne (tafasa su bayan sun ɗebo su daga saƙarsa) ke bin su. Allah shi ne masanin ɓoye amma wannan shi ne abin da jama'a suke hasashe daga yadda abin da suke gani kuma suka lura yana aukuwa na tsawon lokaci.

**6.1.3 Alaƙa da Alharini**

Wani sirri na zaren tsamiya shi ne, zare ne mai daraja da ke da dangantaka da alharini. Alharini nau'in tufafi ne na 'yan Aljannah da aka hana Musulmi, musamman maza sanyawa. Sai dai ko idan za a sa wani ɗan kyallensa ne a haɗa da wani tufafi a ɗinka su tare, domin ƙawata shi.

**7.1 Kammalawa**

Wannan muƙala ta bibiyi lamarin da ya biyo bayan kyautar ƙaho da Mai Martaba Sarkin Kano, Alhaji Aminu Ado Bayero, ya yi wa Shugaban Ƙasa Muhammadu Buhari, kwanakin baya, wato ranar Litinin, 30th January, 2023, domin fayyace tasirin wannan kyauta ta karramawa da Sarakunan Fulani ke yi wa manyan baƙinsu. Muƙalar ta gano abin da ke taskace a cikin ƙahon da aka yi kyautar da shi, wato rigar nan ta alfarma da aka fi sani da *bullan*. Rigar da Sarakuna da attajirai da manyan malaman zaure ke sanyawa. Muƙalar ta tabbatar da cewa, rashin sanin tarihin kyautar ƙahon ya haifar da surutai a ƙasa, da kame-kame na manufar kyautar, musamman a kafafen sada zumunta. Har ta kai ga wasu suka kushe kyautar, domin a ganinsu kamar ƙasƙanci ne a yi wa Shugaban Kasa kyautar ƙaho ba saniya ba. Sannan muƙalar ta tabbatar da matsayi da muhimmancin ƙaho ga al'ummar Hausawa da Fulani da kuma ɗimbin sirrin da ke tattare da zaren tsamiya wanda ake ɗinka *bullan* da shi. Babu shakka waɗannan duk sun bayar da haske kan al'adar naɗe kyautar da aka yi aka zura ta cikin ƙaho domin a burge wanda aka yi dominsa. Haka kuma, muƙalar ta fayyace wasu darajoji da Allah Ya yi wa zaren tsamiya da yadda ake sarrafa shi dalla-dalla tun daga daji har zuwa wurin maɗinkan gargajiya. A ƙarshe muƙalar ta tabbatar da cewa al'adar kyautar ƙaho daɗaɗɗiyar al'ada ce kuma kyauta ce ta isa zuwa ga isassu.

CC BY-NC-ND

**Manazarta**

Abubakar, S.A (1977) *The Lamive of Fombina*. Zaria. ABU Press Limited.
Alhassan da Wasu (1982) *Zaman Hausawa*. Lagos: Islamic Publication Bureau.
Ayuba, A (2013) Kyautayin Bahaushe a Waƙoƙin Baka. Kundin Digiri na Tsakiya, Sashen Harsuna da Al'adun Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.
Baƙo, A (1990) The Socio-Economic History of Sabon- Gari Kano (1913-1989). Unpublished PhD Thesis, Depertment of History: Bayero University.
Dikko. I. da Macciɗo, U (1991) *Kamus Na Adon Maganar Hausa.* Zariya: NNPC Limited.
Garba, S (2020) Karimci da Zaluncin Sarauta a Al'adar Bahaushe: Nazari Daga Wasu Labaran Gasa Ta Farko. Kundin Digiri na Tsakiya, Sashen Harsuna da Al'adun Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.
Gusau, S.M. (2009) *Diwanin Waƙoƙin Baka*. Kano: Century Research and Publication Limited.
Gusau, S. M (2016) *Kamusun Kayan Kiɗan Hausa*. Kano: Century Research and Publication Limited.
Hauwa, M (2008) Karin Harshen Rukuni a Hausa: Nazari a Ƙasar Zazzau. Kundin Digiri na Tsakiya, Sahen Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.
Jauro. U da Muhammad I (2005) *Aade Fulbe*. Kano: T S Ventures.
Maishanu, H.M (2009) The Fulani Traditions of Origins and Migration: A Re-Examination. *Taguwa Journal of Humanities, Vol 2 No. 1.* Katsina: Umaru Musa Yar'adua University.
Mazawaje, M. I (1985) Zambo da Habaici a Waƙar Fada. Kundin Digiri na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.
Kabir, H. K (2017) Al'adar Caahu a Fadar Fulani Ta Kano. Muƙalar da Aka Gabatar a Taron Ƙasa na Ƙara Wa Juna Sani. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Fassara Fasahar Al'umma. Kano: Jami'ar Bayero.
Sallau, B. A (2009) Ƙaura da Shigowar Fulani Ƙasar Hausa da Tasirin Al'adunsu Kan Wanzanci. *Taguwa Journal of Humanities, Vol 2 No. 1.* Katsina: Umaru Musa Yar'adua University. Pp. 142-156.
Umaru, A.N (2008) *Daular Fulani a Kano.* Kano: Benchmark Publishers Limited.
Waya, Z. I (2000) *Kano da Masarautarta Jiya da Yau*. Zariya: Gaskiya Corperation Limited.
Rataye na Daya
Samfurin Hotunan Rigar *Bullan*.

CC BY-NC-ND